# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da

# Tafiye-Tafiye masu ban mamaki na Bulus



**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Janie Forest**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Ruth Klassen**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.**



**Bulus da Silas, ‘yan hidimar Yesu, suna a kurkuku. A’a ba su aikata wani laifi ba – sun kawar da aljanu daga wata mace. Sun nuna gunki – mutane masu sujada wadanda suke a Filifi suna nuna ikon Allah na gaske da Dansa Yesu. Saboda wannan aka kama su, aka bulale su, aka kulle su.**




Za ka iya zato cewa Bulus da Silas za su yi fushi da bakin ciki. Amma ba su yi ba. Maimako, da tsakar dare sai suka zaunasuna wakokin yabo ga Allah! Duka sauran ‘yan kurkukun da masu lura da kurkukun suka ji su.
3


Nan da nan, sai rera wakokin ya tsaya. Allah ya aika da girgizan kasa domin ya girgiza kurkukun. Duka kofofin suka bude. Sarkokin kowa suka tsintsinke.
4


Oh-oh! Mai lura da ‘yan kurkukun ya sani cewa duka ‘yan kurkukun sun gudu a cikin rikicewar. Ko da ma daya ne ya gudu, za a hukunta shi. Abin bakin ciki, sai mai kulle mutane ya ja takobinsa. Zai kashe kansa sai kome ya kare.
5


Amma Bulus ya kira, “Kada ka ji wa kanka rauni, gama dukanmu muna na.” Sa’ad da mai kulle mutane ya gan haka, sai ya ce, “Mallamai, mene ne zan yi don in sami ceto?” Sai suka ce, “Ka ba da gaskiya ga Ubangiji Yesu Kiristi, za ka kuwa sami ceto, da kai da iyalinka.” Cikin farin ciki, mai kulle mutane ya amince.
6


An ‘yantar da su washegari, Bulus da Silas suka yi tafiya zuwa birane masu yawa, suna gaya wa mutane game da Yesu. Wadansu suka ba da gaskiya, wadansu suka yi kokari su ji musu rauni. Amma Allah yana tare da ‘yan hidimarsa. Wata ran da daddare, Bulus ya yi wa’azi na tsawon sa’o’i. Wani saurayi yana zama a fili a bakin taga sai barci ya kama shi. A ganinka mene ne ya faru?
7


Kowa ya sani cewa saurayin ya mutu. Amma Bulus ya sauka kasa ya rungume shi yana cewa “Ransa yana a cikinsa.” Sai suka kawo saurayin da rai, kuma suka kasance da farin ciki sosai.
8

Bulus da Silas sun kasance da samun abubuwa iri-iri yayinda suke tafiye-tafiyensu a Yurob. Abu daya mafi ban mamaki wa Bulus shi ne lokacin da yake a cikin jirgin ruwa. Iri wadannan jirgin ruwan ba na karfe irin na zamani ba, amma na tafiya a ruwa ne wanda hadari da iska mai tsanani yakan tuttura su zuwa nan da can.



9



Bulus yana a cikin jirgin saboda an riga an kama shi kuma. Yanzu dole ya nuna kansa ga shugaba mai mulki a Roma, hedkwata na biranen duniya. Iska mai karfi ya hana jirgin tafiya da sauri. Ya nuna kamar za a yi babbar hadari mai sika a gaba. Wannan tafiya bai yi sumul wa Bulus da sauran 'yan kurkukun tare da masu tukin jirgin ba.

10

"Jama'a, ina gani wannan tafiya zai kare a cikin matsalla," Bulus ya ja musu kunne. Kaftin bai saurare shi ba. Sai ga su suka shiga teku don tafiya. Sa'ad da babba r hadari mai iska ya harbe su, sai suka daddaura igiyoyin kewaye da jirgin don kada ya rabu kashi biyu. Idan jirgin ya karye, kabarin ruwa ga dukansu.



11

Jirgin ya sha jefi nan da can har kaftin na jirgin ya gaya wa kowa ya taimake rage kayansa. A rana ta uku, suka jefar da karfen rige jirgin da zato zai taimaka rage nauyin.



12

Da daddare, mala'ika ya tsaya a gaban Bulus yana gaya masa abubuwan da za su tafi daidai. Sauran sun sami karfafawa daga Bulus sa'ad da ya ce, "Ku kwantar da zuciya, ya ku maza, gama na ba da gaskiya ga Allah cewa komai zai kasance kamar yadda aka gaya mini. Amma dai, dole mu nemi wani wurin da babu ruwa mu dan tsaya a wurin."



13

Bayan 'yan kwanaki, sai iska ya hura jirgin zuwa Malta. Ya faffashe a wurare masu duwatsu ya rabu zuwa kashi-kashi. Kaftin din ya ba da oda ga duk wanda ya iya ruwa ya fito ya tsallake zuwa gaba cikin ruwan su ketare lafiya, wadansu a kwale-kwale wadansu a karyayen gungumen jirgin.



14

A Malta, Allah ya nuna ikonsa. Yayinda suke tattara itace domin kunna wuta, wani maciji ya cije Bulus. Mutanen suka gani kamar zai mutu. Amma cizon macijin bai yi masa komai ba. Sai mutanen suka fara tunani cewa Bulus wani allah ne. Marasa lafiya masu yawa suka zo, kuma Allah ya warkar da su bayan da Bulus ya yi musu addu'a.



15

A karshe Bulus ya isa Roma. Ya dauke su fiye da shekaru biyu kafin a ji kararsa a kotu. Tsakanin wannan lokaci, Bulus ya yi hayan gida yana karban baki. Kun san mene ne Bulus ya gaya wa bakinsa? Mulkin Allah! Ubangiji Yesu Kiristi. Bulus dan hidimar Allah ne a Roma, daidai da duka tafiye-tafiyensa.



16

"Na yi fada mai kyau, na gama tseren, na kiyaye bangaskiyar," Bulus ya rubuta daga Roma. Littafi Mai Tsarki bai gaya mana yadda rayuwarsa ta kare ba, amma wadansu rubucce-rubucce sun ce an kashe shi ta wurin cire masa kai a Roma bisa ga umurnin Sarki Nero. Bulus ya mutu yayinda yake rayuwa a matsayin – dan hidimar Allah mai aminci, wanda yake gaya wa wadansu game da Yesu Kiristi.



17

Tafiye-Tafiye masu ban mamaki na Bulus

Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

a na samu a

Ayyukan Manzani 16, 27, 28

"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130

18



KARSHE

59

60

19

Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.

Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.

Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah: Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.

Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16

20